M
J
A
JU

(١)

## MUTUNTAKA A CIGABAN MUSULUNCI

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, wanda a cikin littafinsa mai girma yake cewa: **(Ya ku mutane ku ji tsoron Ubangijinku da ya halicce ku da rai guda ɗaya..)** [an- Nisa'i: 1], Ina shaida cewa lallai babu abin bauta wa da gaskiya sai Allah shi kaɗai, ba shi da abokin tarayya. Ina kuma shaida cewa lallai shugabanmu, kuma Annabinmu Muhammad bawan Allah ne kuma Manzonsa, Ya Allah Ubangiji ka ƙara masa tsira da aminci da albarka, shi da alayensa da sahabbansa, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har zuwa ranar sakamako, Bayan haka:

Lallai addinin Musulunci ya gina cigaban da ta kai ƙololuwar mutuntaka, da kyawawan ɗabi'u, ya kuma shata wa mutane hanyoyin soyayya, da baiwa, da adalci, gami da daidaito, ta wani zuri na kyawawan ɗabi'u, da cigaba da aikinsu shi ne haɗa kan al'umma ba rarraba ba, suna ginawa ne ba rushewa ba; saboda a sami cikakken tsaro, da aminci, da zaman lafiya, da alhairi ga ɗaukacin mutane.

Lallai cigaban Musulunci ya sami kyawawan ɗabi'unsa ne daga Alƙur'ani mai girma, da Sunnar Annabi mai daraja; saboda a cike suke da kyawawan ɗabi'un mutuntaka masu girma, Allah mai girma da buwaya yana cewa: **(Ya ku mutane, lallai mun halicce ku ne daga namiji da mace, sannan muka sanya kuka zama al'ummomi da ƙabilu masu bambanci da juna, lallai wanda ya fi girma a wurin Allah a cikinku shi ne wanda ya fi ku jin tsoron Allah, lallai Allah yana da masaniya akan komai, babu abin da yake ɓuya masa)** [al- Hujrat: 13], shi ɗan Adam halitta ce mai daraja, saboda irin yanda Allah ya karrama shi, ba kuma tare da la'akari da ƙabilarsa, ko launin fatarsa, ko addininsa

ba, Allah mabuwayin Sarki yana cewa: **(Lallai mun karrama ɗan Adam..)** [al- Isra'i: 70], Manzon Allah (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Dukanku daga Adam kuke, shi kuwa Adam daga turɓaya yake)**, lokacin da ake wuce da wata janaza ta gaban Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam), ya miƙe saboda ya girmama ta, sai aka ce masa: gawar Bayahude ce fa, sai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Ba rai ba ne?!).**

A cikin abubuwan da suke alamta mutuntakar cigaban Musulunci akwai: **tabbatar da 'yancin yin addini ƙarara a fili ta yanda ba zai karɓi tawili ba, da 'yancin gudanar da ibada, da 'yancin kiyaye gidaje da wuraren ibada ga kowa,** ya kuma hana duk wani nau'i na tilastawa, ko tsoratarwa da ta'addanci, Allah mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Shi al'amarin addini babu tilastawa a cikinsa)** [al- Baƙra: 256], haka ma mai girma da ɗaukaka yana cewa: **(Da Ubangijinka ya ga dama da ɗaukacin waɗanda suke a doron ƙasa sun yi imani, yanzu tilasta wa mutane za ka yi har sai sun zama muminai)** [Yunus: 99], haka ma Maɗaukakin Sarki yana cewa: **(Ka tunatar, da ma can ai kai mai tunatarwa ne, ba mai yi masu dole ba)** [al- Ghashiya: 21 – 22], haka ma Allah Maɗaukaki yana cewa: (**Abin da yake a kanka kawai shi ne isar da saƙon da muka ba ka..)** [as- Shura: 48].

A cikin muhimman sassan mutuntakar akwai: **tausaya wa masu rauni, da kuma girmama manya masu shekaru, da kuma bai wa masu fama da naƙasa cikakkun haƙƙoƙinsu ba tare da an tauye masu komai ba,** Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai Allah yana taimakon wannan al'umma ne saboda masu raunin cikinta, saboda addu'ar da suke yi, da sallolin da suke yi, da kuma ikhlasin da suke da**

**shi)**, Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Lallai wanda bai tausaya wa ƙaramin cikinmu ba, bai kuma mutunta babban cikinmu ba, ba shi daga cikinmu)**, lokacin da Sayyiduna Umar Bn al- Khaɗɗab (Allah ya ƙara yarda da shi) ya ga wani tsoho daga cikin Ahlul kitabi, yana bara a wurin mutane, sai ya ce: lallai ba mu yi wa maka adalci a lokacin samartakar ba, idan muka tozartar da kai a lokacin da ka manyanta, sannan ya yanka masa albashi a baitul mali ana ba shi abin da zai ishe, haka ma (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) yana cewa: **(Allah mai yawan rahama yana tausayin masu tausayi, ku tausaya wa waɗanda suke ƙasa da ku, sai Allah wanda yake sama da ku ya tausaya maku).**

****

Godiya ta tabbata ga Allah Ubangijin talikai, tsira da aminci su tabbata ga cikamakin Annabawa da Manzanni, shugabanmu Annabi Muhammadu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) da alayensa da sahabbansa baki ɗaya.

Lallai mutuntakar da take cikin cigaban Musulunci ba ta tsaya wajen yin ta'amuli tare da ɗan Adam kawai ba, sai da da taɓo dangantakar ɗan Adam har da dabbobi, babu abin da yake bayyana haka kaman irin yanda Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya damu a lokacin da ya shiga gidan gonar wani mutum daga cikin mutanen Madina, a lokacin da raƙumi ya kai masa kuka akan abin da mai shi yake yi masa, yana zubar da hawaye, sai Annabi (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya shafe shi ya yi shiru, sai ya ce: **(Wane ne mai wannan raƙumin? Na wane ne wannan raƙumin?)**, sai wani matashi cikin mutanen

Madina ya zo ya ce: nawa ne ya Manzon Allah, sai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Ashe ba za ka ji tsoron Allah game da wannan dabbar da Allah ya mallaka maka ba, lallai ya kawo ƙara gare ni cewa kana azabtar da shi, kana kuma ɗaura masa kaya sama da ƙarfinsa).**

Haka ma Annabinmu (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ga wata tsuntsuwa tare da 'ya'yanta guda biyu, an ɗauke mata ɗanta guda ɗaya, sai (SallalLahu alaiHi wa alihi wa sallam) ya ce: **(Wane ne ya cutar da wannan ta hanyar ɗauke ɗanta? Ku mayar mata da ɗanta).**

Lallai mutane suna matuƙar buƙatar tabbatar da waɗannan ƙa'idoji da kyawawan ɗabi'u na mutuntaka, waɗanda da su ne cigaban addinimu na Musulunci ya bambanta da saura a tsawon tarihi.

**Ya Allah Ubangiji ka ƙara arziki da yalwa a ƙasarmu da sauran ƙasashen duniya.**